(١)

# ALƘUR'ANI MAI GIRMA LITTAFIN RAHAMA GA TALIKAI..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa:

Ma'ana: **(A cikin Alƙur'ani muna saukar da abin da shi ne asalin waraka da rahama ga muminai)** [], haka mai Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Wannan littafi ne mai albarka da muka sauka, saboda haka ku bi shi, ku kuma ji tsoron Allah ko za a yi maku rahama)** [], Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan haka:** Lallai Alƙur'ani mai girma shi ne igiyar Allah mai ƙarfi, shi ne zikiri mai cikakkiyar hikima, duk wanda ya yi magana da abin da ya ƙunsa ya faɗi gaskiya, wanda duk ya yi hukunci da shi kuma ya yi adalci, wanda kuma duk ya yi riƙo da shi za a shiryatar da shi zuwa ga madaidaiciyar hanya, malamai ba sa ƙoshi da shi, kuma abubuwan ban mamakin cikinsa ba sa ƙarewa, kuma ɓata ba ta gegarsa ta kowace fuska, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai wannan Alƙur'ani ne mai girma, a cikin wani taskataccen littafi mai daraja, babu wanda za su shafe shi sai masu tsarki, lallai Ubangijin talikai ne ya saukar da shi)** [].

Alƙur'ani mai girma littafi ne na rahama ga talikai, Allah mai girma yana cewa: **(Ya ku mutane, ku sani cewa lallai wa'azi daga Ubangijinku, da warakar abubuwan da suke cikin zukata, da shiriya, da rahama ga talikai sun zo maku, Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ka ce masu: lallai da falalar Allah, gami da rahamarsa ne ya kamata ku yi farin ciki, wannan shi ne abu mafi alhairi akan abubuwan da suke tattarawa)** [], Allah mai girma yana cewa: **(Mun saukar maka da littafin da yake bayyana komai da komai, kuma shi shiriya da rahama da albishir ne ga Musulmai)** [], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Wannan kam su ne ayoyin Alƙur'ani masu cike da hikimomi, kuma shiriya ne da rahama ga masu kyautatawa)** [], Allah mabuwayi yana cewa: **(Lallai mun zo masu da littafin da muka tsattsara shi akan ilimi, da shiriya, da rahama ga mutanen da suke yin imani)** [].

Kalmar rahama a Alƙur'ani mai girma ta zo sau sama da ɗari biyu, inda Alƙur'ani mai girma ya bayyana rahama a matsayin sifa ce daga cikin sifofin Allah mai girma da buwaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai rahamata ta yalwaci komai da komai)**, haka ma mai girma yana cewa: **(Lallai Ubangijinka shi ne mawadaci mai kuma rahama)** [], yana kuma cewa: **(Rahamar Ubangijinka ta fi abubuwan da suke tattarawa alhairi)** [], haka ma yana cewa: **(Lallai Ubangijinka ya wajabta wa kansa rahama)** [].

Duk wanda yake yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na tadabburi zai riski girman rahamar da Allah mabuwayi yake yi

wa talikai, inda ya halicci dare da rana saboda rahamar da yake yi wa ɗaukacin halittarsa; inda suke hutawa da daddare, su kuma fita neman arziki da raya doron ƙasa da rana, haka ma Allah mai girma da buwaya yana saukar da ruwa daga sama a matsayin rahama ga talikai, Allah mai girma yana cewa: **(A cikin rahamarsa ne ya halitta maku dare da rana, saboda ku sami hutu da natsuwa a cikinsa, ku kuma nemi arzikinsa da falalarsa, saboda ku samu ku yi masa godiya)** [al- Ƙasasi: ٧٣], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Shi ne wanda yake aiko da iska a matsayin albishir kafin rahamarsa ta sauka, har zuwa lokacin da gira-gizai za su ɗauko ruwa mai nauyi, sai su kora su zuwa ga ƙasa matacciya faƙo, sai mu saukar da ruwa a cikinta, sai mu fitar da tsirrai iri- iri na kayan marmari, lallai ku sani cewa: yanda kuka ga haka, to haka muke fitar da matattu, ta yiwu hakan ya sanya ku wa'aztu)** [al- A'arafi: ٥٧].

Lallai Alƙur'ani mai girma ya bayyana cewa Allah ya aiko Manzanni, ya kuma saukar da litattafai ne a matsayin rahama ga talikai, Allah mai girma yana cewa: **(Ko ku ce: da a ce an saukar mana da littafi, da mun fi su shiriya, to lallai hujja daga Ubangijinku da shiriya da rahama sun zo maku)** [al- An'ami: ١٥٧], Allah mai girma ya faɗa wa cikamakon Annabawa da Manzanninsa cewa: **(Ba mu aiko ka ba sai domin ka zama rahama ga talikai)** [al- Anbiya'i: ١٠٧], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai Manzo daga cikinku ya zo maku, duk wani abu da zai wahalar da ku yana**

**damunsa, yana kuma tsananin kwaɗayin kiyaye ku, da ba ku kariya, shi mai tsananin tausayi da rangwame ne ga muminai)** [at- Tauba: ١٢٨].

Haka ma Allah mai girma a cikin Alƙur'ani mai girma ya kira mutane zuwa ga nuna kyakkyawan fata, da sanya rai a cikin rahamarsa, ya kuma bayyana cewa rahamarsa tana kusa da masu kyautatawa, waɗanda suke akan hanyar gaskiya, Allah mai girma yana cewa: **(Ka ce: ya ku bayi na da suka wuce gona da iri akan kawunansu, kada ku kuskura ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah, lallai Allah yana gafarta dukan zunubai, lallai shi mai yawan gafara da rahama ne)** [az- Zumar: ٥٣], haka ma yana cewa: **(Lallai rahamar Allah tana kusa da masu kyautatawa)** [al- A'araf: ٥٦].

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

Babu shakka kan cewa: mumini na gaskiya shi ne wanda yake ɗabi'antuwa da ɗabi'un Alƙur'ani mai girma, wanda Allah ya saukar da shi a matsayin rahama ga talikai, yake kuma ɗabi'antuwa da ɗabi'un Annabi mai girma, wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko shi a matsayin rahama ga talikai, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi sallam) yana cewa: **(Lallai masu tausayi ne Allah mai yawan rahama yake jin tausayinsu, ku tausaya wa waɗanda suke ƙasa da ku, Allah da yake sama da ku sai ya ji tausayinku)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi sallam) yana cewa: **(Allah ya karkasa rahama zuwa gida ɗari, ya riƙe kaso casa'in da tara a wurinsa, ya kuma saukar da kashi ɗaya a doron ƙasa; a cikin wannan kashin ne halittu suke tausayawa junansu, har ta kai ga goɗiya za ta ɗaga kofatonta, gudun kada ta take ɗanta)**, lokacin da raƙumi ya yi bege da shauƙi, ya zubar da hawaye a gaban Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi sallam), sai mai tsira da amince ya ce: **(Wane ne mai wannan raƙumin?)** sai wani matashi daga cikin al- Ansar ya ce: nawa ne ya Manzon Allah, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi sallam) ya ce: **(Ashe bai kamata a ce ka ji tsoron Allah akan haƙƙin wannan dabbar da Allah ya mallaka maka ba? domin lallai ya kawo ƙorarka cewa kana barinsa da yunwa, kana kuma lafta masa kaya)**.

Lallai akwai tsananin buƙatar a ce ɗaukacin mutane sun ɗabi'antu da ɗabi'un Alƙur'ani mai girma, littafin rahama da aminci da zaman lafiya.

Bari mu kammala da jawabai guda biyu, na farko zuwa ga ma'abota Alƙur'ani, na biyun kuma zuwa ga masu hankalin

duniya, muna cewa da ma'abota Alƙur'ani: ku ƙawata Alƙur'ani da muryoyinku, ku jiyar da ɗaukacin duniya Alƙur'ani.. Ya kuma ma'abota Alƙur'ani ya kamata ku ƙawata Alƙur'ani da kyawawan ɗabi'unku, ku sanya martaninku zuwa ga jahilan da suka tauye haƙƙin littafin Ubangijinku ya zama shi ne ƙara bai wa Alƙur'ani mai girma kulawa ta musamman wajen karanta shi, da nazari a cikinsa, da ƙara neman fahimtar ma'anoninsa, da kuma aiki da karantarwarsa.. Ya Allah Ubangiji, duk wanda yake yi wa littafinka makirci, ka mayar da makircin akansa, ka sanya yunƙurinsa ya zama sanadin halakarsa, ka kuma nuna mana cikakken ikonka akansa, ka sanya ya zama aya da izina ga sauran jama'a.

Su kuwa masu hankali na duniya muna cewa da su: lallai duniya ba a shirye take ta ɗauki yaƙe- yaƙe da sunan addini ba, balle kuma yaƙe- yaƙen da suke faruwa, ya kamata ku tashi tsaye ku rungumi shirin yaƙi da dukan nau'o'in ƙiyayya na addini, tun kafin lokacin ya ƙure, duk wani wuce gona da iri, yana haifar da wani wuce gona da irin ne, an riga an kai maƙura sakamakon irin yanda wasu wawaye suka wuce iyaka, inda aka ba su dama haɓaka ƙiyayya, da hura wutar gaba ta addini, wannan kuma yana rushe katangar rayuwar tare, ya kamata a kiyaye.

Lallai babu shakka kan cewa duk Musulmin da yake kishin addininsa yana cutuwa sakamakon duk wani ɓatanci da ake yi wa Annabinsa, ko littafin Ubangijinsa, kuma duk irin yanda masu hankali suka yi riƙo da haƙuri da hikima, da juriya, to

kuwa wata rana wannan hikimar za ta tuƙe, linzamin zai kuɓuce a hannun masu hankali da masu hikima, hakan kuma zai kai mu zuwa ga fitinar da babu wanda ya san ranar tsayawar ta.

**Ya Allah ka amfane mu da abubuwan da Alƙur'ani mai girma ya ƙunsa.**